# Takardar Tantance Tsari da Taswirar Bibiya

Hanyoyin Aiwatar da Tsare-Tsaren Ƙungiya

## Ma'anoni:

**Gwajin Nagartar Tsari:** Waɗannan ƙananan fafutuka ne da aka tsara domin auna matakin shigowar jama'a ta amfani da yanki—walau a rukunin gidaje, ko unguwa, ko wajen aiki. Manufar ita ce a samu gagarumin rinjaye (kashi 75% ko fiye) na masu ba da gudunmuwa a cikin tsarin da aka zaɓa. Yayin wannan gwajin, za ku bibiyi adadin waɗanda suka shiga, wanda hakan zai nuna muku ko kuna SHIRYA yin fafutukar da kuma samun NASARA.

**Jadawalin Taswira:** Waɗannan jerin sunayen kowanne ma'aikaci ne da ke cikin tsarinku, wanda aka tsara bisa yanki, da unguwa, da gidajen zama. Da sauransu. Za ku yi amfani da su wajen lura da yawan mutanen da suka shiga kowane shirin Gwajin Nagarta Tsari.

## Tambayoyin Nazari:

1. Shin a halin yanzu kuna gudanar da shirin Gwajin Nagartar Tsari? Tattauna dabarunku a halin yanzu game da tattara sa hannun jama'a da sauran ayyukan fafutuka. Dangane da abin da kuka koya cikin shirye-shiryen *Organizing for Power*, me za ku so ku sauya? Me ake buƙata don samun gagarumin rinjaye a tsarinku?

2. Shin kuna amfani da Jadawalin Taswira a halin yanzu? Ta yaya jadawalin zai iya ƙarfafa tsarin ayyukan gudanarwarku?

3. Tattauna tsarinku a halin yanzu wajen bibiyar waɗanda suka shiga tsarin, da kuma abin da ku ke son yi daban a nan gaba.

## Tantance Tsarin Wajen Aikinku na Yanzu:

1. Wane irin tsari kuke da shi? Su wanene mutanen da kuke tattarawa a ƙungiyance?

2. Nawa ne jimillar adadin ma'aikatan da ku ke da shi cikin tsarinku?

3. Shin kun taɓa yin wani shirin na Gwajin Nagartar Tsari a baya? Idan kun taɓa yi, waɗanne iri ne?

4. Idan kun yi Gwajin Nagartar Tsari, wanne kaso ne na mutane suka shiga na ƙarshe? Idan kuma ba ku yi ba, wane kaso mafi girma ne na mutanen da suka shiga kowane irin shiri na saka hannu, na gangami ko na ɗaukar matakai a baya-bayan nan?

5. Waɗanne wuraren aiki ne mafi girma da kuke da ƙalubale a kai (wato wurare masu yawan mutane amma masu ƙarancin shigowa aikin)?

6. Waɗanne wuraren aiki ne mafi girma da kuka fi samun nasara cikinsu, kuma mutane nawa ne a kowane wajen aiki?

7. Me za a buƙata don ƙara yawan masu shigowa cikin Gwajin Nagartar Tsari na gaba?

## Gudanar da Gwajin Nagartar Tsarinku na Gaba/ Tsarinku na Farko:

1. Bayan kammala wannan horon, wanne irin Gwajin Nagartar Tsari ne za ku iya gudanarwa a ƙungiyarku?

2. Adadin mutane nawa kuke son cimma?

3. Ganowa tare da kuma shigowa da Jagorori Na gari shi ne GINSHIƘIN nasarar kowane Gwajin Nagartar Tsari. Tsara cikakken shiri da bayanai game da yadda za ku gano, kuma ku shigo da waɗannan jagororin a "sassa mafi girma" da kuka fi fuskantar ƙalubale a ciki.